A Commentary on

# The Forty Hadiths of Imam Nawawi

Imam Abu Zakaria Yahya ibn Sharaf An-Nawawi R.A

شرح الاربعين النووية

للإمام ابو زكريا يحيى ابن شرف النووي

COMMENTARY BY

SUHAIB SIRAJUDIN

# JERIN LITTATTAFAN HADISAI ARBA'IN (40)

**LITTAFI NA BIYU**

**AKAN**

**(FALALAR WADATAR ZUCI, NEMAN HALAL GODIYA GA ALLAH DA ILLOLIN BARA DA ROKO)**

**NA**


SHEHU MANSUR DALA

08029171761

## GABATARWA

Godiya mara iyaka ta ƙara tabbata ga Allah ta'ala a bi sa ni'imomin sa waɗan da ba za su ƙirgu ba. Ya Allah Ka ƙara salati da salami ga shugaban halitta manzon rahama da iyalansa da sahabban sa da masu bin tafarkin su har zuwa ranar ƙiyama.

Wannan shine littafi na biyar a jerin littafan hadisai 40 da nake rubutawa. Sauran sune:

1) Hadisai 40 kan illolin shaye-shaye

2) Hadisai 40 kan illolin zina, luwaɗi, maɗugo da neman dabbobi

3) Hadisai 40 kan falalar bin iyaye da sada zumunci

4) Hadisai 40 kan falalar taimako

Sai kuma wannan da yake hannunka ya kai mai karatu. Ina roƙon Allah ya ba ni iko da ƙarfin gwiwar ci gaba da wannan jere har na kammala adadin da nake fatan kai wa. Ya kuma yaɗa amfaninsu a duk inda masu Magana da harshen Hausa suke a faɗin duniyar nan.

Kamar yadda sunnansa ya bayyana littafin yana Magana kan falalar wadatar zuci, falalar neman halal, falalar godiya ga Allah da kuma illolin bara da roƙo.

Da farko na yi shinfiɗa kan wannan batutuwan domin su taimaka mana mu yi kyakkyawar fahimta ga waɗannan hadisai arba'in sannann kuma mu samu saufiin yin aiki dasu.

Na tabbata idan muka ɗauki waɗannan hadisai muka yi aiki dasu babu shakka za su warware mana matsalolin fatara da mata da ƙasƙanci da kallon raini da ake yi mana a wannan ƙasa ta mu damu samu daraja da ɗaukaka da yalwar arziki da rahamar Allah a lahira.

Allah ka bamu ikon aiki da abinda muka sani - Amin sai mu haɗu a littafi na shi in sha Allah.

**Shehu Mansur Dala**

**Alhamis 1/2/1440 - 11/10/ 2018**

**ABUBUWAN DA SUKE CIKI**

- Gabatarwa
- wadatar Zuci
- Neman Halal
- Godiya ga Allah Ta'ala
- illolin Bara da Rofio
- Hadisai 10 Kan Falalar wadatar Zuci
- Hadisai 12 Kan Falalar Nemman Halal
- Hadisai 18 Kan Falalar Illolin Bara da Rofio
- Kammalawa
- Litattafan da na duba.

## WADATAR ZUCI

Wadatar zuci shi ne babban arziki wanda ba ya fiarewa, wanda ya same shi ya huce haushin duniya ba shi ba hassada ba ganin fiyashi ba bafiin ciki ba ruwan sa da fiulle- fiulle sai ya tankwaɓarwa da wani arzikinsa. Wanda yake da wadatar zuci ya huta shi ne kaɗai ya ke jin daɗin rayuwar sa ya ke cin arzikin sa hankalin sa a kwance.

Wadarta zuci ita ce yarda da gamsuwa da jin daɗi da godiya ga Allah a bisa abinda Allah ya ba ka na ni'imomin sa waɗanda ba su da iyaka misali: Rayuwa, lafiya , Sana'a, Mahalli, Iyali, abin hawa da sauran su, ba tare da hangen abin da wani ko wasu suke da shi ba kuma ba tare da kwaɗayin abin kowa ba. Ita ake kira (Al-fiaratu) da larabci.

Wato dai wadatar zuci ita ce kullum mutum ya dinga duban ni'imomin da Allah yai masa yana jin daɗin su yana duban na fiasa da shi yana godiya ga Allah yana gamsuwa da iya arzikin sa ba ya hangen na wani ballantana ya sa rai ko ya mifia hannun rofio gare shi.

Mai wadatar zuci yana rayuwa cikin 'yanci da mutunci da kuma rufin asiri, yana ji a ran sa ko da an fi shi kuɗi ko mufiamai to shi ma ya fi wani koma ya fi sauran zama lafiya da kwanciyar hankali,

## FA'IDODIN WADATAR ZUCI

Wadatar zuci tana da fa'idodi da amfani mai yawa ga kowanne ɓangare na rayuwar duniya ga mutum a duniyar sa da lahirar sa, wasu daga cikin waɗannan fa'idodin sune:

1) Mai wadatar zuci zai sami yarda Allah Ta'ala

2) Imani baya zama cikakke sai an haɗa da wadatar zuci

3) Mai wadatar zuci yana rayuwa cikin jin daɗi da walwala

4) Mai wadatar zuci ba ya rifie kowa a zuciyarsa wai don ya fi shi wani abun duniya, yana nuna fiauna ga kowa, shi ma yana da farin jini da muhibba a cikin mutane.

5) Imanin sa da yardar sa da hukuncin Allah da amincewar sa da shi da tawakkalin sa kullum daɗuwa suke yi.

6) Ba ya shiga cikin damuwa da ɓacin rai, zuciyar sa a sake take.

7) Wadatar zuci tana hana mutum hassada da annamimanci da yi da mutane.

8) Hanya ce shararriya zuwa al- janna.

9) Allah yana sanya al' barka cikin rayuwar mutum da samun sa.

10) Mutum yana sanin matsayin sa da darajar da Allah yai masa kuma ya kasance mai jan girman sa da mutuncin sa.

11) Yana kasancewa mai godiya ga Allah wacce take sawa Allah ta'ala yai ta ƙarawa mutum ni'imomin sa.

12) Wadatar zuci tana sanya mutum ya kasance mai kamewa ba zai dinga wulaƙantar da kan sa ba wajen bara da karɓe- karɓe

**ABUBUWAN DA SUKE HANA WADATAR ZUCI**

Sai dai kuma duk da waɗannan darajoji da fa'idodi da wadatar zuci ke da su, mutane da dama zukatan su a talauce suke, matattu ne kuma matalauta ne.

To mene ne yake haifar da rashin wadatar zuci?

Akwai dalilai da dama ga kaɗan daga cikin su:

1) Yawan zama da mawadata masu al- mubazzaranci marasa godiya ga Allah marasa wadatar zuci.

2) Tsananin kwaɗayin abin duniya da ƙwallafa rai kan sai an yi rayuwar kece raini da ƙantamawa.

3) ƙarancin karanta al- ƙur'ani da ƙaranci da la'akari da abin da yake koyarwa.

4) Karancin tunanin mutuwa da kwanciyar kabari da lahira, sai ya kasance babu komai a ran mutane masu mataulautan zukata sai hange- hange da lissafin abin wani.

5) Dulmiya cikin sha'awa da biyewar rai kan duk abin da yake so .

6) Son rayuwar bushasha da burga.

**YAYA MUTUM ZAI KASANCE MAI WADATAR ZUCI ?**

1) Wadatuwa da abinda Allah ya baka

2) Karanta rayuwar magabata na fiwarai da gudun duniyar su da wadatar zucin su da koyi da su.

3) Gudanar da rayuwa matsakaiciya ba fiwauro babu kuma al-mubazzaranci.

4) Yawaita Addu'a Allah ya azurta ka da wadatar zuci kamar yadda Manzon Allah (Sallallahu Alaihi Wasallam) yake cewa: "Ya Allah ina rofion ka shiriya, da tafiawa da kamewa da wadatar zuci"

5) Yin cikakken imani cewa kowa a duniyar nan arzikin sa yake ci, tuni Allah ya gama raba arzikin babu yadda za a yi wani ya ci rabon wani.

6) Tursasa zuciya akan yarda rabon ta da arzkin da Allah ya bawa mutum da nisantar kwaɗayi da sa ido akan abin hannun mutane.

7) fiarfafa imani da Allah da amincewa da shi

8) Kullum ka rinfia duban na fiasa da kai, ka da ka rinfia duban na sama da kai.

9) Yarda da cewa Allah ta'ala ya fiaddara lallai sai wani ya fi wani wadata. Tilas ka ga wasu sun fi ka ma kuma ka fi wasu, wasu kuma kun yi dai-dai, haka Allah yai tsarin sa, to ina dalilin damuwa ?

10) Ka yawaita tunanin mutuwa da ziyartar mafiabarta sai ka ji duk abin duniya ma ba ya ɗaɗa ka da fiasa domin fiarshe dai ko me aka samu mutum zai tafi ya bar shi.

11) Yawaita karanta fiur'ani da la'akari da ayoyin da suke magana akan arziki da talauci da kuma hafiifianin ita kan ta duniyar.

12) Ka sani cewa girma da mutunci yana cikin wadatar zuci shi kuwa kwaɗayi da talaucin zuci ba ya haifar da komai sai fiasfianci da wulafianci.

## HIKIMOMI AKAN WADATAR ZUCI

1) Guntun gatarin ka ya fi sari ka ba ni.

2) Rabon kwaɗo ba ya hawa sama.

3) Adon wadata kyauta, adon talaka wadatar zuci

4) Abubuwa biyu ba sa zama guri ɗaya, wadatar zuci da hassada, abubuwa biyu ba sa rabuwa, kwaɗayi da hassada.

5) Mai neman ɗaukaka ya bi Allah, mai neman wadata ya kasance mai wadatar zuci

6) Wadatar zuci ita ce tsan-tsar 'yanci, kwaɗayi shine tsan-tsar bauta.

7) Mai matalauciyar zuciya ba zai taɓa wadatuwa ba har abada.

8) Dutsen da yake hannun ka da shi kake jifa.

9) Kwai a baka ya fi kaza akurki.

10) Duk wanda bai gamsu da kaɗan ba, ba zai gamsu da mai yawa ba.

## KA'IDOJI DA LADABAN NEMAN HALAL

Abu ne sananne ga kowa cewa addinin musulunci bai bar komai ba sai da yayi tanadin yadda yake so a fahimce shi, ko a aikata shi. Neman halal ko kasuwanci da sana'a ginshifii ne a rayuwar mutum saboda haka ba'a bar mutum yayi yadda ya ga dama ba a kasuwanci ko harkokin sana'ar sa.

Da farko an gina tunani da afiidar ɗan kasuwa musulmi akan waɗannan dirkoki:

**1) Dukiya Ta Allah ce:-** Wato mutum ya sani ya kuma yarda cewa duk dukiyar da take cikin duniyar nan da ita kan ta duniyar mallakin Allah ne shi kaɗai. Amma ya baiwa ɗan adam damar amfani da ita a bisa dokakin da ya tsara masa na shari'a. Wato duk abin da kake da shi kamar aro ko ajiya aka baka amma an yarda ka ɗan taɓa dai-dai da tsarin da aka yi maka (Shari'a)

**2) Neman Falalar Allah:-** Duk sana'ar da kake ka dinga yin ta da fatan samun falala daga Allah acikin ta, wato ka yarda Allah shi kadai shine mai bayarwa, kuma shine mai hanawa.

**3) Dogaro Ga Allah:-** Kada ka dogara da wayon ka iyawar ka ko jarin ka ko iyayen gidan ka kawai ka dogara ga Allah shi kaɗai shine mai azurtawa kuma shine mai karɓe arziki yadda ya ke so wanda ya so a lokacin da ya so, kai dai ka yi ƙoƙari da dogara gare shi sai ya taimake ka ya yi maka fiye da yadda kake zato.

**4) Imani da Hisabi:-** Musulmi yayi imani da cewa ranar lahira za a yi masa hisabi kan duk abin da yadda yayi amfani da shi ta hanyar halal ne ko ta hanyar haram? wannan imani zai hana musulmi hauma-hauma da ya- ki -halal- ya - ki - haram a kasuwanci zai kuma hana shi al- mubazzaranci da zalunci da saɓawa Allah ta'ala da dukiyar sa.

**5) Neman Kuɗi ba ya hana bin Allah:-** A kowane hali musulmi yake komai girman hada- hadar sa kada ya mance da dokakin Allah da ambaton sa da kula da ibada musamman sallah. A musulunci babu wani aiki ko sana'a da za a ce ba ruwan Allah da shi, ko kuma ace ai in ba'ai ƙarya ba za a samu komai ba

Akan wadannann diroki ya wajaba dukkan musulmi ya gina harkar neman abincin sa. Allah yasa mu dace.Amin.

Bayan haka ga fa'idojin neman halal a musulunci a taƙaice

**1) A kaucewa Riba a kowanne Hali:-** Allah ta'ala ya haramta riba da duk wata mu'amala da take da alaƙa da riba. Manzon Allah (Sallallahu Alaihi Wasallam) yace: Allah ya la'anci mai cin riba, da mai ciyar da ita, da mai rubuta ta, da masu shaida a kan ta yace duk matsayin su ɗaya" Muslim ne ya ruwaito shi.

**2) An haramta Algus da Ha'inci da yaudara:-** Duk wani nau'i na ha'inci da yaudara, zamba da cin amana haramun ne a kasuwanci. Manzon Allah (Sallallahu Alaihi Wasallam) yace: wanda yayi mana algus ba ya daga cikin mu (Muslim ne ya ruwaito shi)

Hanyoyin ha'inci da algus suna da yawa kaɗan daga cikin su sune:

1) Sayar da kaya marasa inganci da waɗanda lokacin amfaninsu ya fiare (expiring date)

2) Tauye mudu da ma'auni da rage nagartar abin sanyarwa (quality).

3) Sanya tsofaffin kaya a cikin sabbin kwalaye da ledoji da gyara su zama kamar sababbi a yi musu kuɗin sababbi.

4) Sayar da duk wani abu da yake cutarwa ga lafiya da rayuwar ɗan adam da dabbobi da tsirrai.

5) Bayannan fiarya da zigwigwita kayan sayarwa don kawai a jawo hankalin mai saye musamman magunguna.

6) Ha'inci a wajen gini ta hanyar rage sumunti, ko rodi a yi ginin da nan da nan zai tsatstsage ko ma ya ruguje.

(2) Kaucewa duk wani aiki na haram ko wani abu da aka haramta amfani da shi a kasuwanci.

Iri-iren waɗannan harkoki suna da yawa kaɗan daga cikin su sune:

1) Haramta saye da sayar da giya da dukkanin kayan maye.

2) Saye da sayar da fina-finan batsa da mujalla da hotuna da duk wani abu da yake yaɗa ɓarna da ta'addanci.

3) Keɓantar ta sakatariya wannan haramun ne, haka ma duk kasancewar ta sakatariya wannan haramun ne, haka ma duk wani aiki ko sana'ar da sai mace ta bayyana jikin ta sannan za ta yi ta.

4) San'ar raye -raye da kaɗe –kaɗe da wasannin kwaikwayo da duk masu hannu a ciki irin su mai ba da umarni, mai ɗaukar hoto, mai kwalliya, mai fiir- fiirar labari, mai bada kufii , mai tsara wafia, mai rerawa da sauran su.

Na san wasu za su ga wannan hukuncin kamar yayi zafi to tambaya a nan gare su ita ce shin a musulunci wasan kwaikwayo (film) yana daga cikin uzurin ko dalili da suke halatta bayyana tsiraici yin fiarya? shin yana halatta keɓantar mace da wanda

ba muharramin ta ba? shin wasan kwaikwayo zai iya halatta ɗimbin ayyukan saboda Allah da keta alfarmar shari'a da kyawawan ɗabi'o'i har ma a ce wai sana'a ce ta faɗakarwa da ilimantarwa?

Ni dai a iya ɗan karatuna wanda bai kai ko rabin cikin cokali ba da kuma gurguwar fahimta ta ban ga inda film zai iya halatta haramun ba. Sai dai ance fahimta fuska?

5) Saye da sayarwa da dillancin kayan sata da na fiwace duk wannan haramun ne. Haramun ne saye da sayar da duk wani abu da yake cutarwa ga hankali da lafiyar mutane da zaman lafiyar su.

Duk wata sana'a ko harka da ta fiunshi zamba, yaudara, ha'inci, algus da rashin tabbas (garari) kan abin saye ko kuɗin wannan ma haramun ne.

Waɗannan kaɗan ne daga fia'idodin kasuwanci a musulunci sai mu kula ko ma samu albarkar neman mu.

Su kuwa ladaban kasuwanci wato ɗabi'u da halaye da ya kamata duk wani ɗan kasuwa ko mai sana'a ko ma'aikaci ya siffantu da su, sune:

1. Kyakkyawar niyya ya kasance niyyar sa da burin sa a wanan harka da yake yi mai kyau ce.
2. Fita akan lokacin zuwa kasuwa ko gurin sana'a ko aiki. Manzon Allah (Sallallahu Alaihi Wasallam) ya rofii Allah ya sa albarka a harkar masu zuwa a akan lokaci ban da masu makara.
3. Ambaton Allah lokacin shiga kasuwa sai ka ce: la ilaha illallahu wahdahu la sharika lahu lahul mulku wa lahul hamdu yuhyi wa yumitum wa huwa ala kulli sha'in fiadir.
4. Yiwa mutane sallama da amsa sallamar su a wurin sana'a ko kasuwa.
5. Saufii da rangwame yayin saye da sayarwa da biyan bashi ko karɓar bashi da yin sassauci ko afuwa ga wanda yake cikin fiunci.
6. Gakiya da amana babu abin da yake na bunfiasa kasuwanci da kowacce harka sama da gaskiya da rifion amana.

7. Sifantuwa da kyawawan halaye kamar hafiuri, kyauta, kunya, godiya da sauransu.
8. Cika mudu da ma'auni da bin fia'idojin aiki sau da fiafa da inganta sana'a da kyautata ta.
9. Yawaita ba da sadaka da fitar da zakka idan dukiya ta kai kuma lokaci yayi.
10. Cika al'fiawari ban da fiarya, ban da yaudara.
11. Ka guji yawan rantsuwa ko da akan gaskiya ne ballantana akan fiarya.
12. Kada ka bada cin hanci kuma kada ka karɓa.
13. Ka guji duk wata mu'amala ta cuta da haram.
14. Ka kula da sallah da sauran dokokin musulunci.
15. Ka guji saɓawa Allah a gurin nema kamar zina da luwaɗi shaye-sheye da sauransu.
16. Ka kasance mai tsafta a jikin ka da gurin sana'ar ka da abin sayarwarka ka fiawata shi.
17. Ka kasance mai sakin fuska da magana mai daɗi ga duk wanda hulɗa ta haɗa ka da shi.
18. Ka kai zuciyar ka nesa ka denne zuciyar ka, ka guji saurin fushi da hasala.
19. Ka dogara ga Allah shi kaɗai ka yi ta godiya a gare shi, ka yi ta rofion sa ka yi ta ambaton sa.
20. Ka mayar da hankalin ka akan sana'ar ka duk abin da bai shafe ka ba ka rabu da shi.

Duk ɗan kasuwa ko ma'aikaci ko mai sana'ar da ya kula da waɗannan fia'idoji da ladabai hafiifia Allah ta'ala zai sanya masa albarka a cikin neman sa.

Allah ta'ala ya taimaka mana. Amin.

## GODIYA GA ALLAH TA'ALA

Mutum ba zai kasance mai wadatar zuci da neman halal da kaucewa rofio da barace - barace ba har sai ya kasance mai godiya ga Allah Ta'ala.

Hafiifianin godiya ga Allah shine bayyana ni'imar Allah ga bawa a harshe ta hanyar yabo da kirari da gode masa a fili da ɓoye da jin girman ni'imomin da gamsuwa da su a cikin zuciya da nuna fiauna gare su da kuma bin Allah da waɗannan ni'momin da bayyana su ga mutane.

Wannan shine abinda ake kira godiya ga Allah wato (ASHSHUKURU) misali a nan shine: A matsayin ka na ɗan kasuwa ko mai fian-fiantar jarin ka, ko ma'aikaci komai fiaranci al'bashin ka, ko mai sana'a ko mai fian-fiantar ta godiyar ka ga Allah ita ce:

Ka rinka jin daɗi da gamsuwa da fiauna da godewa Allah kan wannan aiki ko sana'a da ya baka, saboda ai akwai miliyoyin ka da basu da aiki ko sana'a. Ka bayyana falalar da Allah yai maka, ka sa kaya masu kyau ka ci mai kyau ka yalwatawa kanka da iyalin ka ba tare da almubazzaranci ba.

Ka rinka fadar baiwar da Allah yai maka, kan gode masa kada kullum ka yi ta kuka kana nuna cewa babu wani abu da Allah ya yi maka.

Ka yi biyayya ga Allah da wannan ni'ima da Allah ya yi maka, ka bi dokoki da fia'idojin aikin ko sana'ar ka yi taimako ka yi sadaka ka bi ladaban kasuwanci ko sana'ar. Wannan shi ake kira godiya ga Allah ta'ala

Godiya ga Allah ta'ala tana da falala da ɗumbin fa'idodi masu yawa waɗanda suka haɗa da:

1. Godiya ga Allah ta'ala ita ce rabin imani.
2. Godiya ga Allah ta'ala tana sa mutum ya samu yardar Allah a duniya da lahira.
3. Godiya ga Allah ta'ala alama ce cikakkiya kuma ingantacciya ta bautar Allah.
4. Godiya ga Allah ta'ala siface kuma ɗabi'a ce ta annabawa Alaihimussalam.

5. Godiya ga Allah ta'ala sifa ce kuma Ɗabi'a ce ta 'yan al-jannah
6. Godiya ga Allah ita ce sirrin dawwamar ni'imomin Allah da fiarkon su da fiaruwar su.

Abubuwan da suke taimakon mutum ya kasance mai godiya ga Allah ta'ala su ne:

1. Ka yarda da gamsuwa da abin da Allah ta'ala ya ba ka, ka daina fushi da yadda Allah yayi ka da abin da ya ba ka.
2. A kullum ka rinfia duban ni'imomin Allah a gare ka waɗanda ba za su fiirgu ba misali: Halitta, lafiya, ji, gani,magana, bacci, ci, sha, suttura, ilimi, sana'a, da sauransu.
3. Ka rinfia kallon na fiasa da kai ka daina kallon na sama da kai, sai ka ga ashe kai ma ba a baya kake ba.
4. Ka rinfia karanta labaran masu godiya ga Allah kamar annabawa da salihan bayi, kuma ka yi koyi da su.
5. Sanin falalar godiya ga Allah da illolin butulce masa da rashin godiya a gare shi.
6. Baya- baya da duniya da fiarantar kwaɗayin abin duniya.

**ILLOLIN KARƁE-KARƁE DA BARACE-BARACE**

Addinin musulunci addini ne da ya girmama ɗan adam ya mutunta shi ya kuma yi umarni da ya kare mutuncinsa ya girmama kansa kada ya wulafianta kan sa da kan sa ya zubar da fiimar sa ta ɗan adam.

Domin tabbatar da wannan manufa Allah ta'ala ya umarci kowa ya tashi ya zage dantse wajen neman na kan sa ya yi umarni ya kasance mai wadatar zuci da godiya ga Allah ta'ala, kuma ya hana bara, rofio, maula, banbaɗanci da sauran su.

Wannan ɗabi'a ce mummuna wacce take kashe zuciyar mutum ta haifar masa da talauci da fiasfiancin a duniya da lahira. A duniya talauci zai aure shi ya mamaye shi, a lahira kuma zai tashi babu tsokar nama ko ɗaya a fuskar sa.

Duk abin da mai karɓe- karɓe yake samu haramun ne tsantsa sai dai in yana da wani dalili da shari'a ta yarda shi wanda ya halatta masa yin roƙon kamar yadda za'a kawo hadisai da suke magana akan hakan.

Ya Allah ka ba mu wadatar zuci ka ba mu ikon godiya a gare ka da dagewa wajen neman halal ka tsare mu da cin haram da zubar da mutunci mu wajen roƙe-roƙe. Amin Summa Amin.

## HADISAI GOMA AKAN WADATAR ZUCI

### HADISI NA DAYA

An karɓo daga Abdullahi ɗan Amr (Radiyallahu Anhuma) Haƙiƙa Manzon Allah (Sallallahu Alaihi Wasallama) yace: " Haƙiƙa wanda ya musulunta kuma aka azurta shi da gwargwadon buƙatarsa, kuma Allah ya ba shi wadatar da abinda ya bashi, ya samu babban rabo."

Muslim ne (1045) ya rawaito shi.

A wata ruwaya wacce Tirimizi da Hakim suka rawaito daga Fadalata bin Ubaidin haƙiƙa Manzon Allah (Sallallahu Alaihi Wasallama) yana cewa: "Farin ciki ya tabbata ga wanda aka shirye shi zuwa ga musulunci, kuma samunsa ya kasance gwargwadon buƙata, kuma ya wadatu.

### KARIN BAYANI

Haƙiƙa duk wanda Allah ya yi shi musulmi kuma yana rayuwa cikin rufin asiri gwargwadon buƙata shi ba talaka can ƙasa ba shi kuma ba mawadaci na sama ba, sannan ya samu gamsuwa da wadata da godiyar Allah ga wannan yanayi da yake ciki, to haƙiƙa wannan ya samu nutsuwa da farin ciki da kwanciyar hankali. Saboda haka wanda yake cikin irin wannan hali sai ya yi ta godiya ga Allah kada ya tayarwa da kansa hankali ta hanyar kwaɗayi da hange - hange.

## HADISI NA BIYU

An karbo daga Sahl ɗan Sa'ad (Radiyyalhu Anhu) ya ce: " Ya Muhammad ka rayu yadda kake so, hafiifia kai za ka mutu, kuma ka aikata abinda ka so, hafiifia za a yi maka sakamako da shi, kuma ka so duk wanda ka ga dama, hafiifia za ka rabu da shi, kuma ka san hafiifia ɗaukakar mumini shi ne tsayuwarsa da daddare, bayarwarsa shi ne wadatuwarsa ga mutane.

Ɗabarani ne ya ruwaito shi da kyakkaywa isnadi.

## KARAIN BAYANI

Wannan hadisi ya fiunshi muhimman ginshifiai na samun nasara a rayuwa ba ta duniya kawai ba, har ma da ta alfiiyama.

Ga tafiaitattun bayanai a kansa:

1. Ya kamata mutum ya yi wa kansa hisabi ya tambayi kansa shin wane irin salo na rayuwa yake bi? Saboda ko ba daɗe ko ba jima sai ya mutu ya bar wannan duniya. To in da hankali ya kamata a yi rayuwa mai tsafta kafin zuwan mutuwa wacce dole sai ta zo.
2. Dukkannin aikin da kake aikatawa Allah yana jin ka yana ganin ka ko alhairi ko sharri, yi fiofiari ka yi alhairi.
3. Duk wata haɗuwa fiarshenta rabuwa. Saboda haka ka yi nazari su wane ne abokan hulɗarka, waɗanda kake fiauna? In mutanen kirki ne a ci gaba da hulɗa, in na wofi ne, ka yi watsi da su, tun kafin a rabu baran-baran ana la'antar juna da jefawa juna laifi.
4. Kiyamullaili wato sallar nafila cikin dare yana kawo wa mutane kwarjini da girma a wurin mutane.
5. Kame kai da barin rofie- rofie da kwaɗayin abin hannun mutane yana sanya mutum ya zama mai mutunci da girma a idon mutane saɓanin mai karɓe-karɓe, wanda ba shi da wani girma ballanta muhibba a idon mutane har fiananan mutane ma sai su raina shi.

Ya kamata 'yan' uwa mu yi la'akari sosai da koyarwar wannan hadisi mu rinfia tafiyar da rayuwarmu da mu'amalolinmu akansa.

**HADISI NA UKU**

An karɓo daga Abu Hurairah (Raidallahu Anhu) daga Annabi (Sallallahu Alaihi Wasallam) ya ce: " Yawan dukiya ba shi ne wadata ba,hafiifiar wadata ita ce wadatar zuci."

Bukhari (6081) Da Muslim 4140 ne suka ruwaito shi.

**KARIN BAYANI**

Allahu Akbar hafiifia wannan tafiaitaccen hadisi cike yake da ɗimbin fasaha da hikima da bayanin hafiifianin yadda al'amura suke.

Mutane da yawa suna ɗaukar tarin kuɗi da kadarori shi ne arziki da wadata, ko da kuwa mai su yana da talakar zuciya matsiyaciya. A gaskiya abin ba haka ba ne, za ka samu talaka mai wadatar zuci hankalinsa a kwance, ransa a sake jikinsa garau fuskarsa fes, yana cikin walwala da nishaɗi babu abinda ya dame shi, rayuwarsa cikin tsari da lissafi abin gwanin ban sha'awa.

Shi kuwa mai kuɗi amma yana ɗauke da matalauciyar zuciya kullum cikin fiunci yake ba shi da wani hutu, ba fara'a ba walwala, ba ya ji a ransa cewa shi mawadaci ne ballantana ya godewa Allah, ga shi da tsananin hassada da bafiar mugunta da ɗankaran ganin fiyashi da kuma mashahuriyar rowa. Jininsa da sukarinsa kullum a sama suke, haka lafiyarsa gaba ɗaya a taɓarɓare take, amma fa ga damin kuɗi da gidaje da motoci da sauransu waɗanda shi kansa bai san yawansu ba, bai kuma san me zai yi da su ba. Shin ɗan'uwa ina arziki ko jin daɗi anan?

Ya Allah ka ba mu wadatar zuci.Amin.

Hadisi na gaba ya fiara fito mana da ma'anar wannan hadisi.

## HADISI NA HUƊU

An karɓo daga Abu Zarrin (Radiyallahu Anhu ) ya ce: Manzon Allah(Sallallahu Alaihi Wasallam) ya ce da ni: "Ya kai Abu Zarr shin kana ganin yawan kuɗi shi ne wadata? Sai ne ce i, ya ma'akin Allah. Sai ya ce: Shin kana ganin fiarancin kuɗi shi ne talauci? Sai na ce: Na'am ya ma'akikin Allah. Sai ya ce:" Wadata ita ce wadatar zuci kawai, talauci shine shi ne talaucin zuci kawai."

Ibn Habban ne ya rawaito shi.

## HADISI NA BIYAR

An karɓo daga Abu Hurairah (Radiyallahu Anhu)ya ce: Manzon Allah (Sallallahu Alaihi Wasallam) ya ce: "Ku dubi na fiasa ba za ku raina ni'imar Allah ba a gare ku.

Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi.

A wata rawayar ta Bukhari ya ce: Idan ɗayanku ya ga wanda aka fifita shi a kansa da dukiya ko kyawun hilitta, to ya dubi na fiasa da shi.

## KARIN BAYANI

Da kowa zai rinfia yin aiki da wannan hadisi da duniya ta zauna lafiya, da ba a yi hassada da gaba da aikata munanan laifuka ba don kawai a samu kuɗi.

Allah Ta'ala cikin hikimarsa ya tsara rayuwar mutane hawa - hawa akwai na can sama, akwai na tsakiya akwai kuma na fiasa. a duk matakin da kake sai ka ga na sama da kai da wanda kuke daidai da na fiasa da kai. To in kana duban na fiasa da kai sai ka godewa Allah ka ji cewa ko ba komai kai ma dai ka fi waɗansu.

Wannan zai hana ka jin haushin na sama da kai da tunanin sai ka cutar da su, zai kuma hana ka yin fushi da hukuncin Allah sannan kuma za ka ji gamsuwa a ranka da gwargwadon abinda Allah ya ba ka, ba kuma ba za ka raina waɗanda ka fi ba.

Lallai wannan hadisin maganin matsaloli ne masu yawa.

**HADISI NA SHIDA**

An karɓo daga Abul Abbas Sahal ɗan Sa'ad Assa'idi (Radiyallahu Anhu) yace: Wani mutum ya zo wurin Annabi (Sallahu Alaihi Wasallam) ya ce: Ya Ma'aikin Allah sanar da ni, abin da Allah zai so ni, sai ya ce:"Ka guji duniya sai Allah ya so ka, kuma ka guji abin hannun mutane sai mutane su so ka."

Ibn Majah ne da waninsa suka rawaito shi da isnadai masu kyau.

**KARIN BAYANI**

Ma'anar gudun duniya shi baya- baya da ita da rashin sanya ta a rai ta yadda abin duniya ko nemansa ba zai rufe maka ido ba ya hana ka bin Allah ko ya sa ka rowa, ko ya sa ka fi bayar da hafifiofiin da suka wajaba a kanka kamar zakka, zumunci da ciyar da iyali.

Gudun abin hannun mutane yana nufin kame kai da nisantar kwaɗayin abin hannunsu da wadatuwa da abin da Allah Ta'ala ya azurta ka da shi.

Wannan ɗabi'u guda biyu: Gudun duniya da gudun abin hannun mutane duk wanda ya ɗauke su a matsayin hanyar rayuwar hafiifia Allah Ta'ala zai so shi, sannan kuma mutane ma za su so shi ya zama mai farin jini da kwarjini da muhibba da kuma mutunci a cikinsu.

**HADISI NA BAKWAI**

An karɓo daga Ubaidullahi ɗan Mihasan (Radiyallahu Anhu) ya ce: Manzon Allah (Sallallahu Alaihi Wasallam) ya ce: " Wanda ya wayi gari a cikinku yana amintacce cikin jama'arsa, jikinsa lafiya, yana da abinda zai ci a yininsa, to hafiifia shi kamar wanda aka tattarowa duniya ne gaba ki ɗayanta.

Tirmizi ne ya rawaito shi ya ce hadisi ne kyakkayawa.

**KARAN BAYANI**

Duk kuɗin mutum idan yana cikin tashin hankali da rashin zaman lafiya, ko kuma yana kwance sharaf ba lafiya, ai talakan da yake zaune lafiya, kuma jikinsa fialau ya fi shi. Saboda da za a ce da mai kuɗin ya bayar da dukiyarsa don ya samu lafiya

ko tsaro a guje zai bayar. Ashe ke nan lafiya da tsaro sun fi kuɗi daraja. Kuma duk tarin kuɗin mutum bufiatar wannan ranar kaɗai zai iya yi da dukaiyarsa kamar yadda talaka ma zai yi. Don ba zai ci abincin kwana uku ba a lokaci guda saboda tafiamar wadata, ba zai sa kaya kala biyar ba da sauransu.

Ashe kenan talakan da Allah ya ba shi lafiya da zama lafiya da ɗan abinda za a jalatu sai ya godewa Allah, da shi da sarkin duniya duk matsayinsu ɗaya.

**HADISI NA TAKWAS**

An karɗo daga Hasan (Radiyallahu Anhu) ya ce: Manzon Allah (Sallallahu Alaihi Wasallam) ya ce: " Mafi alhairin arziki shi ne gwargwandon bufiata."

**KARIN BAYANI**

Ma'ana mafi alhairin arziki shi ne Allah ya azurta mutum da rufin asiri da rayuwa matsakaiciya, ba cen sama ba, ba fiasa ba.

**HADISI NA TARA**

An karɓo daga Abdullahi ɗan Umar (Radiyallahu Anhu) ya ce: Manzon Allah (Sallallahu Alaihi Wasallam) ya taɓa kafaɗata sai ya ce: "Ka kasance kamar bafio a duniya, ko kamar matafiyi." Abdullahi dan Umar ya kasance yana cewa idan ka kai yamma, kada ka sa rai za ka kai safiya. Idan ka wayi gari kada ka sa rai zakka kai yamma. Ka ribaci lafiyarka kafin rashi lafiyarka, kuma ka ribaci rayuwarka kafin mutuwarka.

Bukhari ne ya rawaito shi.

**KARIN BAYANI**

Hafiifia wannan wasiyya ta Manzon Allah (Sallallahu Alaihi Wasallam) tana fiunshe da fia'idojin zaman lafiya da samun wadatar zuci. Tana koya mana mu wadatu da gargwadon bufiatarmu kada mu tayar da hakulanmu wajen neman abinda ya fi fiarfin bufiatunmu. Mu yi rayuwa irin ta bafii da matafiya, saboda shi bafio da matafiyi ba ya sakin jiki ya yi ta fantamawa ta yadda guzurinsa zai fiare ya rasa mafita.

Sannan kuma shi Ibn Umar sai ya zuzzurfar fahimata ga wannan wasiyya ya ce ka yi amfani da dama ta lafiya da rayuwa wajen aikin alhairi, maimakon hanfioran tara abin duniya, fiarshe mutuwa ta zo kwatsam, ko rashin lafiya ya dabaibaye mutum daga nan sai nadama marasa iyaka. Ya Allah ka bamu ikon amfana da damar da ka ba mu a rayuwarmu kafin ta kuɓuce mana.

## HADISI NA GOMA

An karɓo daga abu Hurairah (Radiyallahu Anhu) Hafiifia Manzon Allah (Sallaallahu Alaihi Wasallam) ya ce: " Ba miskini ba ne wanda loma ɗaya ko loma biyu za ta juyar da shi, ko dabino biyu. Amma miskini shine wanda ba ya samun abinda zai wadatar da shi, kuma ba a fahimaci halin da yake cikin ba, ballanta a ba shi sadaka, shi kuma ba zai iya tashi ya rofii mutane ba.

Bukhari da Muslim ne suke rawaito shi.

## KARIN BAYANI

Wannan hadisi yabo ne ga mutumin da yake mai kame kai da wadatar zuci wanda yana cikin matsala da bufiata amma kuma ba zai iya rofion mutane ba, kuma ba kowane yake iya sanin halin da yake ciki ba, wannan shi ne wanda ya kamata a koda yaushe a rinfia taimakawa ba mu su yawo suna Ala- ba- Ku- Mu- samu ba ana ɗan watsa musu suna tsincewa wasu ma a hakan sun fi masu ba su sadakar kuɗi.

## HADISAI 12 KAN FALALAR NEMAN HALAL

## HADISI NA GOMA SHA ƊAYA

An karɓo daga Mikdam bin Ma'adi Yakriba (Radiyallahu Anhu) daga Annabi (Sallallahu Alaihi Wasallam) ya ce: "Ɗan Adam bai ci abinci mafi alhairi ba fiya da wanda ya samu daga aikin hannunsa. Kuma hafiifia Annabin Allah Dawuda ya kasance yana cin abincin da ya samu daga aikin hannunsa."

Buhari (1966) ne da Ibn Majah suka rawaito shi. A ruwarya Ibn Majah yace: "Babu sana'a mafi tsarki irin sana'ar hannu. Kuma duk abinda mutum ya kashe domin ciyar da kansa da iyalansa da 'ya' yansa da 'yan aikinsa za a ba shi ladan sadaka.

**KARANI BAYANI**

Allah Ta'ala ya sanya ɗimbin albarka da rufin asiri cikin sana'ar hannu, muddin an kaucewa ha'inci saɓa alfiawari da cuta sannan kuma an kwantar da hankali an yarda da gamsuwa da abinda Allah ya bayar.

**HADISI NA GOMA SHA BIYU**

An karbo daga ka'ab ɗan Ujarh (Radiyallahu Anhu) ya ce: " Wani mutum ya wuce Annabi (Sallahu Alaih Wasallam) sai sahabban Annabi suka ga fiarfin da kazar-kazar ɗinsa, sai suka ce ya Ma'aikin Allah ina ma da a ce wannan fiarfin nasa da kazar- kazar a wajen jihadi yake amfani da shi ba wajen neman duniya ba? Sai Manzon Allah (Sallallahu Alaihi Wasallam) ya ce: "Idan ya fito ne, domin nemawa 'ya'yansa fianana abinci, ai shi ma aikin Allah ne, kuma in ya fito ne domin ya ciyar da iyayensa tsofaffi, shi ma aikin Allah ne, in ya fito ne domin ya ciyar da kansa, ya kame kansa daga rofio shi ma aikin Allah ne, idan kuwa ya fito ne saboda ya samu abin da zai yi riya da alfahari da shi, to hafiifia aikin shaiɗan ya ke yi.

Ɗabarani ne ya rawaito shi, kuma masu ruwayarsa amintattu ne.

**KARIN BAYANI**

Waɗansu mutane sukan ɗauka cewa yin sana'a ko aiki ko kasuwanci domin neman halal ɗin da mutum zai rifie kansa da iyalansa da iyayensa da shi, kamar wani aiki ne na duniya, wanda ba shi da wata dangantaka da lahira.

Wannann fahimta ba haka take ba kuskure ne. Saboda Allah Ta'ala shi ne ya yi umarni a nemi halal a kula da hafifiofiin iyalai da na iyaye da na mutum shi kansa, ashe duk hanyar da za a bi domin sauke wannan nuyin indai ana bin dokokin Allah a cikinsa ta shi ma ibada ne wanda Allah yake ba da lada a kansa.

**HADISI NA GOMA SHA UKU**

An karɓo daga Zubairu ɗan Awwam (Radiyallahu Anhu) ya ce: Manzon Allah (Sallallahu Alaihi Wasallam) ya ce: Mutum ya ɗauki igiya ya tafi daji ya yi ice, ya ɗoro a bayansa ya sayar ya tsare mutuncinsa ya fi alhairi a gare shi da ya rinfia rofion mutane ko su ba shi ko su hana shi."

Bukhari da muslim ne suka ruwaito shi.

**KARIN BAYANI**

Komai fianfiantar sana'a ta fi alhairi ga mutum akan ya kasance mai matacciyar zuciya ya yi ta rofion mutane, koda kuwa za su ba shi.

Wannan hadisi kwaɗaitarwa ne akan lallai ne musulmi ya tashi tsaye ya nemi na kansa kada ya raina fiaramar sana'a.

**HADISI NA GOMA SHA HUƊU**

An karɓo daga Abdullahi ɗan Umar (Radiyallahu Anhuma) ya ce:An tambayi Manzon Allah (Sallallahu Alaihi Wasallam) wacce sana'a ce mafificiya? Sai yace: Sana'ar hannu da dukkan cinikin da babu haram a cikinsa."

Tabarani ne ya ruwaito shi a cikin Mu'ujamul Kabir da Mu'ujamul Asaut, waɗanda suka ruwaito shi amintattua ne.

**HADISI NA GOMA SHA BIYAR**

An karɓo daga Abu Hurairah (Radiyallahu Anhu) ya ce: Manzon Allah (Sallallahu Alaihi Wasallam) ya ce:" Hafiifia Allah Ta'ala mai tsarki ne, ba ya karɓar (Sadaka/Zakka) sai wace aka yi da tsarkakkiyar dukiya. Kuma Allah ya umarci muminai da abinda ya umarci manzanni da shi, sai ya ce: " Ya ku manzanni ku ci halal ku yi ayyuka managarta hafiifia ni masani ne da abin da kuke aikatawa." Kuma ya ce: "Ya ku wanɗan suka yi imani ku ci daga halal ɗin da muka azurta ku da shi. Sai ya ba da labarin wani mutum wanda ya yi doguwar tafiya, ya yi ciɗin-ciɗin ya yi busu- busu yana ɗaga hanayensa sama yana cewa ya Ubangiji, ya Ubangiji, alhali haram yake ci, haram yake sha, haram yake sa wa, kuma an ciyar da shi da haram, to ta fiafia za a amsa addu'ar wannan?

Muslim da Tirmizi ne suka rawaito shi.

## KARIN BAYANI

Wannan hadisi ya fiunshi falalar neman halal da cin halal ta fuskoki kamar haka:

1. Su kansu manzanni an umarce su da neman da kuma cin halal haka su ma sauran muminai, wato gama- garin mutane sun yi tarayya da manzanni a cikin wannan umarni.
2. Allah Ta'ala yana amsa addu'ar mai nema halal da cin halal. Shi kuwa mai amfani da haram a cinsa da shansa da tufarsa da sauransu, Allah ba ya amsa addu'ar sa koda kuwa ya cika sharaɗan karɓar addu'ar, saboda cin halal shi ma yana cikin sharaɗan karɓar addu'ar.
3. Kwaɗaitarwa kan neman halal da tsawatarwa kan cin haram.

## HADISI NA GOMA SHA SHIDA

An karɓo daga Abdullahi ɗan Amr (Radiyallahu Anhuma) hafiifia Manzon Allah (Sallallahu Alaihi Wasallam) ya ce: "Idin kana da halaye huɗu kada ka damu da abinda ka rasa na duniya: "Rifion amana, gaskiyar magana, kakkyawar halitta da kamewa a wajen cin (abinci)."

Ahmad da Ɗabarani ne suka rawaito shi, kuma isnadinsu kyawawa ne.

## KARIN BAYANI

Waɗannan ɗabi'u guda huɗu ni'ima ce mai girma.Rifion amana gaskiya, kyawun halitta da kuma cin halal, wanda ya same su kada ya damu don ba shi da tarin abin duniya.

## HADISI NA GOMA SHA BAKWAI

An karɓo daga Abu Hurairah (Radiyallahu Anhu) ya ce: Hafiifia Annabi (Sallallahu Alaihi Wasallam) ya ce: "Idan ka bayar da Zakkar dukiyarka hafiifia ka sauke wajibin da kanka. Kuma duk wanda ya tara dukiyar haram ya yi sadaka da ita, ba za a ba shi lada ba, kuma nauyi bai sauka ba daga kansa.

Iban Huzaima da Ibn Hibban da Hakim ne suka rawaito shi.

## KARIN BAYANI

- Zakka ita ce babban hafifiin dukiya da yake kan mutum, duk sauran abubuwa na kyautatawa a bayan zakka suke.

- Yin sadaka da dukiyar haram ba ya sa a yafewa mutum zunubin wannan haramcin, kuma ba zai samu ladan wannan sadakar ba, saboda haka mu dage mu nemi halal kuma ku yi alhairi da halal.

## HADISI NA GOMA SHA TAKWAS

An karɓo daga Abu Huraira (Radiyallahu Anhu) hafiifia Manzon Allah (Sallallahu Alaihi Wasallam) ya ce: " Zamani zai zo wanda mutum ba zai damu da abinda ya ya samu ba ta hanyar halal ne ko hanyar haram.

Bukhari da Nasa'i ne suka rawaito shi.

## KARIN BAYANI

Hafiifia halin ya- ki- halal- ya- ki- haram mummunan hali ne da mutane za su tsunduma a cikinsa a fiarshen zamani wanda Manzon Allah (Sallallahu Alaihi Wasallam) yake yi mana gargaɗi da zuwa wannan lokaci. Lokaci ne da musibu da laifuffuka za su yawaita su ta 'azzara su gurɓata rayuwar kowa, saboda kowa zai haukace shi sai ya yi kuɗi ta kowane hali. Allah ya kyauta.

## HADISI NA GOMA SHA TARA

An karɓo daga Abu Hurairah (Radiyallahu Anhu) ya ce: An tambayi Manzon Allah (Sallallahu Alaihi Wasallam) kan abinda ya fi shigar da mutane wuta? Sai ya ce: Cikin da farji. Kuma an tambaye shi kan abinda ya fi shigar da mutane aljanna? Sai ya ce: "Tsoron Allah da kyawawan halaye."

Tirmizi ne ya rawaito shi.

## KARIN BAYANI

Cin haram da zinace- zinace da maɗigo da luwaɗi da saduwa da dabbobi da gumaka su ne zunuban da za su yi sanadiyyar shigar ɗinbin mutane cikin wuta.

A yayinda kyawawanan ɗabi'u irinsu gaskiya, amana, taimako cika alfiawari da sauransu da kuma bin dokokin Allah da kaucewa abubuwan da ya hana su ne sanadin shiga aljannan ga mutane da yawa. Allah ka sa mu a cikinsu Amin.

## HADISI NA ASHIRIN

An karɓo daga Mu'azu (Radiyallahu Anhu ) daga Annabi (Sallallahu Alaihi Wasallam) ya ce: "Kafafuwan bawa baza su bar siraɗi ba sai an yi masa tambaya kan abubuwa guda huɗu: A kan rayuwarsa a cikin me ya fiarar da ita? Da kuruciyarsa yaya ya tsufar da ita, da dukiyarsa ta wacce hanya ya same ta kuma ta wacce hanya ya kashe ta? Da iliminsa shin ya yi aiki da shi?

Baihafii ne ya rawaito shi da waninsa.

## KARIN BAYANI

Lallai ne mutum ya kula da lokacinsa musamman lokacin fiuruciya da samartaka ya tabbatar yana kakkyawan amfani da shi wajen aika ayyukan alhairi waɗanda za su amfane shi a duniyarsa da lahirarsa.

Haka kuma duk abinda zai nema ya tabbata ya bi ta hanya mai kyau ta halal ba haram ba, kuma in ya samu ban da almubazzaranci banda fiwauro. Sannan Lallai ne ya rinfia yin aiki da abinda ya sani na liimin addini da inganta rayuwa.

Waɗannan abubuwa ne muhimmai wanda tun a duniya aka inganta su, in aka je lahira suna da matsala to fa mutum ba zai tsira ba Allah ya kiyaye.

## HADISI NA ASHIRIN DA ƊAYA

An karfio daga Ka'abu ɗan Ujrata (Radiyallahu Anhu) ya ce Manzon Allah (Sallallahu Alaihi Wasallam) ya ce da ni: "Ya kai Ka'abu ɗan Ujrata hafiifia nama da jinin da suka tsiro ta hanyar haramun wuta ce ta fi cancanta ta cinye shi. Ya kai Ka'abu ɗan Ujrata mutane masu wayar gari irin biyu ne: akwai mai wayar gari ya

'yanta kansa, akwai kuma mai wayar gari wanda zai halakar da kansa.

Tirmizi da Ibn Habban ne Suka rawaito Shi.

**KARIN BAYANI**

- Duk nama da jini da ya taru a jikin mutum ta hanyar cin haramun to hafiifia wutar jahannama aka kiwatawa kawai, sai a guji, fiiba da kyan jiki da haramun.

- Kullum gari ya waye kafin yamma waɗansu sukan fanshi kawunansu daga wuta ta hanyar ayyukan alhairi,, waɗansu kuma sukan halaka kansu ta hanyar saɓo da zalunci. Sai mutum ya yi nazari ya yiwa kansa hisabi a kullum ya daga safe zuwa dare 'yanta kansa ya yi, ko kuwa halaka kansa ya yi.

**HADISI NA ASHIRIN DA BIYU**

An karɓo daga Abubakar Assiddik (Radiyallahu Anhu)daga Annabi (Sallallahu Alaihi Wasallam)ya ce: Duk jikin da aka ciyar da shi da haram ba zai shiga aljanna ba."

Abu Ya'ala da Bazzar da Ɗabarani ne suka rawaito shi.

**KARIN BAYANI**

Wannan hadisi tsoratarwa ce mai girman gaske kan cin haramun da nuna cewa wuta ce kadai za ta cinye jikin da aka ciyar da shi aka kiwata shi da abincin haram. Ya Allah ka ba mu ikon cin halal ka tsare da haram.

**HADISAI 18 KAN ILLOLIN BARA DA ROKO**

**HADISI NA ASHIRIN DA UKU**

An Karɓo daga Abdullahi ɗan Umar (Radiyallahu Anhuma) hafiifia Manzon Allah (Sallallhu Alaihi Wasallam) ya ce: "Rofio ba zai fiyale ɗayanku ba har sai ya haɗu da Allah Ta'ala babu ko tsokar nama a fuskarsa."

Buhari da Muslim da Nasa'i ne suka rawaito shi.

## KARIN BAYANI

Ma'anar wannan hadisi shi ne muddini mutum yana roke- roke da barace-barace to a koda yaushe mutuncinsa da darajarsa zubewa suke yi da haka har ya mutu ya je lahira ba shi da wata daraja, fuskarsa sai gashi kwarangwal ba nama, duk ya cinye shi a wajen karbe- karbe. Wannan ita ce somin tabi na zabar da za a fara yi masa karin kuma a jefa shi a wuta. Allah ya kiyaye mu.

## HADISI NA ASHIRIN DA HUƊU

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas (Radiyallahu Anhuma)ya ce: Manzon Allah (Sallallahu Alihi Wasallam) ya ce:" Duk wanda yake rofion mutane ba tare da wani talauci da ya afka masa ba, ko iyali da ya kasa ɗaukar nauyinsu ba, zai zo ranar fiiyama babu nama a fuskarsa.

Baihafii ne ya rawaito shi.

## HADISI NA ASHIRIN DA BIYAR

An karɓo daga Ibn Abbas (Radiyallahu Anhuma) ya ce: Manzon Allah (Sallahallahu Alaihi Wasallam) ya ce: "Duk wanda ya buɗewa kansa fiofar rofio ba tare da wani talauci da ya afka masa ba, ko iyali da ya kasa daukar nuyinsu, Allah zai buɗe masa kofar talauci da fatar ta inda ba yazo."

Baihafii ne ya rawaito shi.

## KARIN BAYANI

Karayar ariziki wacce za ta jefa mutum cikin halin gigitar rayuwa da shi da iyalansa tana halattawa mutum yin rofio har dai zuwa lokacin da Allah zai kawo masa saufii sai ya daina mifia hannunsa ga kowa.

Amma in ba da wannan dalili ba, duk wanda ya mayar da rofio ko bara sana'a, to ya jefa kansa cikin kuttun fatar da tsiya maras yankewa.

## HADISI NA ASHIRIN DA SHIDA

An karɓo daga A'iz ɗan Amr (Radiyallahu Anhu): Hafiifia wani mutum ya zo wurin Manzon Allah (Sallahu Alaihi Wasallam) ya rofie shi ya ba shi. Da ya sa kafarsa a dandamalin fiofa sai Manzon Allah (Sallallahu Alaih Wasallam) yace: Da sun san abinda yake cikin rofio da wani bai tafi wurin wani ba yana rofionsa.

Nasa'i ne ya rawaito shi.

## KARIN BAYANI

Wannan mutumin yana bara ne ba tare da wata lalura ba, sai dai ya mayar da ita sana'a, shi ne sai Ma'aikin Allah (Sallallahu Alaih Wasallam) ya ce: "Da irin waɗannan mutane sun san hatsarin dake cikin rofio da bara da babu wanda zai je ya rofii wani. Amma rashin sani, ko take sanin ko raunin imani shi yake sanya masu matattun zukatu bara da rofio.

## HADISI NA ASHIRIN DA BAKWAI

An karɓo daga Sauban (Radiyallahu Anhu) ya ce: Hafiifia Annabi (Sallallhu Alaihi Wasallam) ya ce: "Duk wanda ya rofii wani abu alhali ya fi fiarfin abun, to wannan abun zai kasance wani mummunan tabo a fuskarsa ranar fiiyama.

Ahmad da Bazzar da Dabarani ne suka rawaito shi.

## KARIN BAYANI

Akwai mutane masu tsananin kwaɗayi da son banza, za ka gan su suna zubar da mutuncinsu suna 'yar murya don a ba su abinda sun fi fiarfinsa nesa ba kusa ba, saboda nasu shi ne mai daraja na wasu kuwa banza ne. Su a tananinsu dabara suke yi, amma ina? Ga shi Manzon Allah(Sallallahu Alaihi Wasallam) ya ce: za su tashi da mumman tabo a fuskokinsu na waɗannan abubuwan da suka rofia.

## HADISI NA ASHIRIN DA TAKWAS

An karɓo daga Mas'ud ɗan Amr daga Annabi (Sallallahu Alaihi Wasallam) Hafiifia an kawo masa wani mutum da ya mutu domin ya yi masa salla, sai ya tambaya ya ce nawa ya bari? Sai suka ce: Ya bar dinare biyu ko uku: Sai ya ce: "Ya bar

abubuwa biyu ko uku da za a yi masa sakiya da su a wuta.

Baihafii ne ya rawaito shi.

**KARIN BAYANI**

Ɗaya daga cikin masu ruwayar hadisin nan ya ce: Na huɗu da Abdullahi ɗan Kasim bawan Abubakar sai na gaya masa wannan hadisin sai ya ce: Wannan mutumin ya kasance yana bara ne don kawai ya tara kuɗi."

Wato wannan mutumin ya mayar da bara sana'a duk da hanin da Manzon Allah (Sallallahu Alaihi Wasallam) ya yi a haka har ya tara dinare uku, sai Manzon Allah (Sallallahu Alaihi Wasallam) ya ce: "Za a sa su a wuta su yi zafi a yi ta dadana masa a jikinsa ranar fiiyama. Wato irin azabar da za a yi wa mawadata masu hana zakka za a yi masa.

Yakamata masu wannan hali su daina. Saboda sai irinsu sun mutu a yi ta mamakin abinda suka bari wanda a barar suka tara shi. Tir da su.

**HADISI NA ASHIRIN DA TARA**

An karɓo daga Hushi ɗan junadata (Radiyallahu Anhu) ya ce: "Na ji Manzon Allah (Sallallahu Alaihi Wasallam) yana cewa:Duk wanda yake bara/rofio ba tare da lalura ba, to hafiifia shi kamar yana cin garwashin wuta ne.

Ɗabarani da Ibn Huzaima da Baihafii ne suka rawaito Shi.

**KARIN BAYANI**

Masu bara da rofio don kawai lalaci da son banza to su sani wuta balbal suke ci, in ji Manzon Allah (Sallallahu Alaihi Wasallam). A yi hattara!

**HADISI NA TALATIN**

An karɓo daga Hubshi ɗan junadata (Radiyallahu Anhu) ya ce: Na ji Manzon Allah (Sallallahu Alaih Wasallam) a lokacin hajjin ban kwana yana tsaye a Arafa sai wani bafiauye ya zo wurinsa ya kama gafen mayafinsa ya rofie shi ya ba shi, sai ya cire ya ba shi. Ya karɓa ya tafi.

Sai Manzon Allah (Sallallahu Alaihi Wasallam) ya ce: "Rofio ba ya halatta ga mawadaci, ba ya halatta ga fiafifiarfa lafiyayye, sai dai wanda talauci ya durfiusar da shi, ko ba shi ya yi masa kanta. Duk wanda yake rofion mutane don ya tara kuɗi, wannan abinda ya samu zai kasance wani mummunan tabo a fuskarsa ranar fiiyama, kuma za a mayar da shi konannen dutse da zai rinfia cinsa na Jahannanma.

Saboda haka wanda ya so ya karɓa da yawa, wanda ya so ya karɓo kaɗan.

Saboda haka wanda yakarɓa da yawa, wanda ya karɓo kaɗan.

Tirmizi ne ya rawaito shi.

Razin ma ya ruwaito shi a tasa rayuwar ya fiara da cewa: Sai Manzon Allah (Sallallahu Alaihi Wasallam) ya ce: "Hafiifia akan baiwa mutum abu, ya karɓa ya makale shi a hammatarsa, alhali wuta ya karba. Sai Umar ya ce To ya Ma'aikin Allah me ya sa kake ba da abin da yake na wuta? Sai ya ce: "Ni dai Allah ya hana ni rowa, su kumu sun fii, su daina rofiona".

Sai sahabbai suka ce: Mece ce gwargwandon wadatar da in mutum yana da ita bai halatta ya yi rofio ba? Sai ya ce in dai yana da abincin safe ko abincin dare (to shi mawadaci ne).

**KARIN BAYANI**

Wannan hadisin yana bayanan wasu daga cikin waɗanda ya halatta su yi rofio/bara wato wanda talauci ya durfiusar da shi ya nukurkusa shi har ya rasa inda zai sa kansa, amma da zarar sun samu waraka to haramun ne su ci gaba da rofio.

Wanda kuwa yake da lafiyarsa da fiarfinsa kuma ba ya cikin halin ni – 'yasu to duk abinda ya samu a bara ko rofio wuta balbal ya ke ci.

**HADISI NA TALATIN DA ƊAYA**

An karɓo daga Abu Abdurrahman Auf ɗan Malik Al'ashaja'i (Radiyyallahu Anhu) ya ce: Mun kasance a wurin Manzon Allah (Sallallahu Alaihi Wasallam) mu tara ko takwas ko bakwai sai yace: Shi ba za ku yi wa Manzon Allah (Sallallahu Alaihi

Wasallam) mubaya'a ba? A lokacin ba mu dađe da yin mubaya'a ba. Sai muka ce: Ai mun yi maka mubaya'a ya Ma'aikin Allah. Sannan sai ya ce: " Shin ba za ku yi wa Manzon Allah mubaya'a ba?" Sai muka shimfiđa hanayenmu muka ce hafiifia mun yi maka mubaya'a ya Ma'akin Allah, shin akan me za mu yi maka mubaya'a? Sai ya ce: "Ku bautawa Allah shi kađai kada ku yi shirka, ku yi salloli biyar, ku yi biyayya, sai ya fadi wata kalma a ɓoye. kuma Kada ku rofii mutane komai.

Hafiifia na ga wađansu daga cikin irin wađannan mutane bulalarsa tana fađowa amma ba zai rofii wani ya miko masa ita ba.

**KARIN BAYANI**

Mubaya'a shi na caffa wato alfiawari da yarjejeniyar biyayya ga shugabanni akan yi haka ta hanyar musafaha da shi da hanyoyi da aka bi, a bisa bambancin al'adu.

Muhimmanci sanin ciwon kai ya kai ga har ma'aikain Allah (Sallallahu Alaihi Wasallam) ya hađa rashin rofio da Tauhidi da sallah, kuma su sahabbai sun kasance komai fianfiantar rofio ba sa yin sa.

**HADISI NA TALATIN DA BIYU**

An karɓo daga Abu Zarrin (Radiyallahu Anhu) ya ce: Masoyina Manzon Allah (Sallallahu Alaihi Wasallam) ya yi min wasiyya da abubuwa bakwai:

1) Son miskinai da jan su a jiki.

2) Na rinfia duban na fiasa da ni, na daina duban na sama da ni.

3) Na rinfia sadar da zumunta koda kuwa đan'uwa ya nisance ni.

4) Na rinfia yawan fađar lahaula wala fiuwwata illa billahi.

5) Na rinfia fadar gaskiya komai đacinta.

6) Kada na ji tsoron zargin mai akan lamarin Allah.

7) Kan na rofii kowa komai.

Ahmad da Đabarani ne suka rawaito shi.

Hafiifia waɗannan wasiyyoyi guda bakwai sun tattaro alhairai masu ɗimbin yawa waɗanda in mutum ya yi aiki da su zai zauna lafiya da kowa kuma zai samu sanyin rai da rayuwa mai daɗi.

## HADISI NA TALATIN DA UKU

An karɓo daga Saubau (Radiyallahu Anhu) ya ce Manzon Allah (Sallallahu Alaihi Wasallam) ya ce: "Duk wanda ya lamunce min cewa ba zai rofii mutane komai ba, zan lamunce masa shiga aljanna.

Ahmad da Nisa'i da Ibn Majah da Abu Dawud ne suka rawaito shi.

## KARIN BAYANI

Lallai lamarin dogaro da kai ya kai matufia a musulunci ta yadda Manzon Allah ya yi alfiawarin aljanna ga duk wanda yake da hafiuri da kame kai wanda ba ya rofion mutane komai. Saboda haka shi Sauban sahabin da ya rawaito hadisin, in bulalarsa ta faɗo daga kan dokinsa, sai ya sauko ya ɗauka ba zai ce da wani ya miko masa ba.

## HADISI NA TALATIN DA HUƊU

An karɓo daga Abu Bishirin Kabisatu ɗan Muharifiu (Radiyallahu Anhu) yace: Na ɗauki wani lamuni sai na je wurin Manzon Allah (Sallallahu Alaihi Wasallam) ina rofionsa ya taimaka min na biya. Sai ya ce to ka saurara sai an kawo zakka sai mu ba da umarni a ba ka wani abu. Sannan sai ya ce ya kai Kabisatu rofio ba ya halatta sai ga ɗayan mutum uku:

1) Mutumin da ya ɗauki wani lamuni, rofio, ya halatta a gare shi har ya samu abinda zai biyu daga nan sai ya daina rofion.

2) Mutumin da wata musiba ta afkawa dukiyarsa ta fiare gaba ɗaya, ya halatta ya yi rofio har ya samu abinda zai rifie rayuwarsa (jari)

3) Mutumin da talauci ya afka masa ta yadda har mutane uku masu hankali za su fahimci halin da yake ciki su ce lallai babu ta afkawa wane shi ma ya halatta ya yi rofio har ya samu abinda zai rifie rayuwarsa.

Amma bayan waɗannan ka sani ya Kabisatu duk wanda ya yi rofio tsantar haramun yake ci.

Muslim da Abu dawud da Nasa'i ne suka rawaito shi.

**KARIN BAYANI**

Lamuni shi ne mutum ya ɗauki nauyin zai biya wani ba shi ko wata diyya ko wasu kuɗi da aka yi sulhu akansu domin kaucewa wata fitina tsakanin mutane, to idan mutum ya ɗauki irin wannan nauyin sai kuma ya gaza to ya halatta ya yi rofio har ya samu abin da zai biya wannan kuɗi daga nan kuma sai ya dakata da rofion.

**HADISI NA TALATIN DA BIYAR**

An karɓo daga Abu Hurairah (Radiyallahu Anhu) daga Annabi (Sallallahu Alaihi Wasllam) ya ce: "Bawa ba zai kasance mai cikakken imani ba sai mafiocinsa ya amincewa sharrinsa, kuma wanda ya ba da gaskiya da Allah da ranar lahira ya girmama bafionsa, wanda ya yi imani da Allah da ranar lahira ya faɗi alhairi ko ya yi shiru. Hafiifia Allah Ta'ala yana son mutum mai wadatar zuci, mai hafiuri mai kame kai. kuma yana fiin mutum mai batsa, fajiri mai rofie- rofie da naci.

**HADISI NA TALATIN DA SHIDA**

An karɓo daga Abu Sa'id Alkhudri (Radiyallahu Anhu) hafiifia waɗansu mutanen Madina sun rofii Manzon Allah (Sallallahu Alaihi Wasallam)ya ba su, har sai da duk abinda yake da shi ya fiare, sai ya ce: "Duk abinda nake da shi na alkairi ba zan ɓoye na hana ku ba, wanda yake fiofiarin kame kai Allah zai ba shi kamewa, wanda yake fiofiarin ya kasance mai wadatar zuci, Allah zai ba shi wadatar zuci, wanda yake fiofiarin yin hafiuri Allah zai ba shi hafiuri kuma babu wata kyauta da Allah ya yiwa wani sama da hafiuri.

Malik da Buhari da Muslim da wasunsu ne suka rawaito shi.

## KARIN BAYANI

**-** Wannan hadisin yana nuna kyawun hali na Manzon Allah (Sallallahu Alaihi Wasallam) na hafiuri da yawan kyauta.

**-** Wadatar zuci da kame kai da hafiuri ɗabi'o'i da sai mutum ya hori zuciyarsa akansu ta yadda za su zama jiki da ɗabi'a a gare shi. Sai a yi fiofiarin yafiar zuciya da juriya da nisanta munanan halaye.

**-** Ɗabi'ar hakuri ce ɗabi'a mafi girma da alhairi da muhimmanci a komai na rayuwa.

## HADISI NA TALATIN DA BAKWAI

An karɓo daga Abdullahi ɗan Mas'ud (Radiyallahu Anhu)ya ce: Manzon Allah (Sallallahu Alaihi Wasallam) ya ce wanda wata lalura ta matsi ta saukar masa sai ya kai kukansa ga mutane ba za a magance masa wannan talauci ba, wanda kuma ya kai kukansa ga Allah ba da jimawa ba Allah zai kawo masa arziki ko a kusa ko a nesa

Tirmizi da Abu Dawud da Hakim ne suka rawaito shi.

## KARIN BAYANI

Duk mutumin da ba shi da wani aiki sai fiarar Allah ga mutane da yawan mita da koke- koke to hafiifia zai dawwama cikin talauci da fatara. Wanda kuwa ya koma ga Allah yake ta kai kukansa yana rofionsa to ko ba daɗe ko ba jima Allah zai azurta shi.

## HADISI NA TALATIN DA TAKWAS

An karɓo daga Mu'wiyya (Rdiyallahu Anhu) ya ce: Manzon Allah (Sallahllahu Alaihi Wasallam) ya ce: "kada ku nace a cikin rofio, saboda na rantse da Allah duk wanda ya rofie ni wani abu na bashi ba da daɗin rai na ba, Allah ba zai sa masa albarka ba a cikinsa.

Muslim da Nasa'i Hakim ne suka rawaito shi.

## KARIN BAYANI

Hafiifia masu rofie- rofie waɗanda ake ba su ba da ɗin rai ba sai don tsananin nacinsu ko don gudun sharrinsu, haramun suke ci kuma Allah ba zai sanya albarka ba a cikin abinda suke samu. Saboda haka ya zama wajibi kan kowa ya dage ya nemi na kansa.

## HADISI NA TALATIN DA TARA

An karɓo daga Abu Musal ASh'asari (Radiyallahu Anhu) hafiifia ya ji Manzon Allah (Sallahllahu Alaihi Wasallam) yana cewa: "Tsinanne ne wanda yake yin rofio da girman Allah, kuma tsinannane ne wanda aka rofie shi alfasha ne.

Ɗabarani ne ya rawaito shi.

## KARIN BAYANI

Abinda mabarata da masu rofie-rofie suke yi na cewa "a ba su don Allah", don girman zati, da amfani da kalmomi na addini kamar zikiri, madahu da sauransu duka haramun ne kuma ci da addini ne, da raina girma Allah aljanna ce kawai ake rofionta don girman Allah ita kuma ba a rofionta a wurin kowa sai Allah.

Sai gashi kuma in an rofie ka a wannan sigar kuma ba saɓon Allah ba ne, kaya da zunubin yana kan wanda ya karɓa.

## GODIYA GA WANDA YA BAYAR

## HADISI NA ARBA'IN

An karɓo daga Nu'umanu ɗan Bashi (Radiyallahu Anhu) ya ce: Manzon Allah (Sallallahu Alaihi Wasallam) ya ce: "Wanda bai godewa kaɗan ba, ba zai godewa mai yawa ba, wanda bai, godewa mutane ba, ba zai godewa Allah ba, bayyana ni'imar Allah godiya ce barin bayyanawa butulci, ne haɗin kai rahama ce, rarrabuwa azaba ce.

Abdullahi ɗan Imam Ahmad ne ya rawaito shi a cikin littafin "Zawa'id" da Ibn Abid Duniya a cikin littafin Isadina'ul Ma'aruf".

## KARIN BAYANI

- Idan wani ya yi maka alhairi komai ƙanƙantarsa ka godewa wanda ya yi maka, bayan ka godewa Allah Ta'ala.
- In Allah ya ba ka kada ka yi butulci ka ɓoye ka nuna sam kai ba ka da komai wannan zai gaggauto maka fushin Allah wanda zai sa ya kwace abinda ya baka.
- Amfanin haɗin kai da illar rarrabuwa.

## KAMMALAWA

Haƙiƙa duk wanda ya karanta wannan littafi daga farko har ƙarshe ya ga matsayin shugaban halitta kan batutuwan wadatar zuci, neman halal, godiya ga Allah da kuma bara da roƙo.

Babu yadda za'ai musulmai mu ci gaba a wannan duniya mu samu girma da daraja sannan kuma mu samu rahama Allah a lahira sai fa mun bi koyarwar manzon mu Sallallahu Alaihi Wasallam sau da ƙafa.

Sai mun rabu da lalaci son banza da tumasanci da maula da bara sannan kuma mun wadatu da gamsuwa da abinda muka yi gumi muka samu sannan martabarmu da ita da za ta dawo. Amma matuƙar muka ci gaba da zama akan waɗancan miyagun halaiya to haƙiƙa duk wani ci gaba sai dai mu gani ana yi wani ma ko matsayin 'yan kallo ba za su samu ba.

Ya kamata malamai musamman na makarantun boko da na islamiyya a kowanne mataki su rinƙa yaɗa irin waɗannan hadisai da koyar da su, sannan kuma hukumomi su fito da hanyoyi na gaskiya tabbatattu na yaƙi da fatar ba hanyoyin yanbara ba waɗanda suke share wurin zaman dirshan ga fataratar da talauci malamai su nuna koyi ga al'umma ta hanyar kame kai da wadatar zuci da kau da kai daga abun hannun mutane da gujewa karɓe-karɓe da sauran hanyoyin damfara da ci da addini.

Allah ka taimake mu ka bamu ikon aiki da abin da muka sani. Godiya a gare ku da kuke karanta rubutu na kuma ina neman addu'ar ku da kuma gayran kura-kurai na da shawar- wari.

Na gode. Mu haɗu a littafi na gaba da izinin Allah.

Abu Muhammad Addalawi (Shehu Mansur) Dala.

Alhamis 23/2/1440 = 1/11/2018

**LITTATTAFAN DA NA DUBA**

1) Sahihut Targib Wattarhb- Mhammad Nasiruddini Al- albani (Rahimahullah), Maktabatul Ma'arif Riyad, 1421/2000.

2) Fikhut Tajrihi Muslim wa Aadaadubhu - Farfesa Husamuddin Musa Affana - Makatabatu Dindis - Falastin - 2006.

3) Sirru Dawamin Ni'am - Dakta Falasal bin Mish'al Aal Su'ud - Maktabatul Aadaab - Alkahira - 2013.

4) Mafhumun Ni'mah Fil Kur'ani Karim Wal Hadisin Nabawi Assharif - Farfesa Abdulmajid bin Mas'ud - Darussalam - Misra 1432/2011.

**5) www.islamway.net**

6) **www.mawdoo3**.com_